# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Ni ma ɗan Adam ne: 'Yan Afirkan da ke fama da taɓin hankali
## Kashi na bakwai: Abin da ya jawo


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Chrispin Mwakideu |
| Wanda ya fassara: | Yusuf Idris |
| Wadda ta tace: | Halima C. Schmaling |


**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Duduwa: | 'yar shekara 35 |
| Likita: | ɗan shekara 50 |
| Amina: | 'yar shekara 19 |
| Dije: | 'yar shekara 19 |
| John: | ɗan shekara 25 |
| Mudi: | ɗan shekara 50 |

**Mai gabatarwa:**

Masu sauraronmu, barkanmu da sake saduwa da ku a cikin kashi na bakwai na shirinmu na “Ji Ka Karu” wanda muke kawo muku a kan mutane masu fama da ciwon taɓin hankali a ƙasashenmu na Afirka. A cikin shirin da ya gabata mun ji yadda jama’a ke ƙyaman masu taɓin hankali da nuna bambanci tsakaninsu da wasu marasa lafiyan. Amma daga ina aka samu irin wannan rashin sanin, da ƙyama, da kuma rashin tausaya wa masu taɓin hankali? Za mu ji amsa a cikin shirin namu na yau mai taken “Abin da ya jawo”. Za mu faro ne daga inda Duduwa da ɗanta Musa suka je ganin wani likita a birni mai suna Dr. Mudi.

**Fitowa ta 1: A asibiti**

**Likita:** Na gaba ya shigo!

**Duduwa:** Likita ina kwana?

**Likita:** Lafiya ƙalau, Malama. Me ya faru?

**Duduwa:** Likita, na kawo maka ɗana ne. Sunanshi Musa. Ban san yadda zan yi maka bayanin al’amarin ba. Amma ni dai ina ganin aljanu ne suke damunshi, amma kuma ban san abin da ya sa suka zaɓe shi ba. Na kawo maka shi ne saboda ka taimake shi, ni ma kuma ka taimake ni. Saboda na yi iya ƙoƙarina amma har yanzu ban ci nasara ba.

**Likita:** Mhm. To, ki faɗa min ainihin abin da yake damunshi. Kuma me ya sa kike tunanin cewa bai da hankali?

**Duduwa:** Na ɗaya dai yanzu shekarunshi goma sha shida, amma har yanzu maganarshi ba ta fita sosai. Kuma idan ma yana magana wani lokaci, da ƙyar za ka gane abin da yake cewa,

musamman ma idan ya tsorata, ko kuma ya yi fushi, da kuma idan abin ya tashi. Sai ka ga yana ta maimaita abu ɗaya, sannan ba ya son kowa ya je kusa da shi, kuma ba shi da abokai. Sai dai ya yi ta zama shi ɗaya, kuma ba ya canzawa.

**Likita:** Yaushe ya fara yin haka? Sannan za ki iya tuna lokacin da kika fara ganin alamomin haka?

**Duduwa:** Na fara tunanin cewa akwai abin da yake damunshi lokacin da ya cika shekara ɗaya da rabi. Da can ba abin da yake damunshi, amma kuma kawai sai ya fara manta wasu abubuwan da ya koya, ba ya cuɗanya da kowa, ba ya son ya riƙa wasa, sannan ba ya iya magana kamar yadda ya kamata, da dai sauransu. Ni kuma sai na yi tunanin cewa wani abu ne da zai wuce, zai warke ya ci gaba da gudanar da rayuwarsa kamar kowa, amma hakan bai faru ba. Tun shekara goma sha huɗu da suka wuce na kasance cikin wahala da ƙunci saboda halin da yake ciki.

**Likita:** To ina ganin daga abin da kika faɗa min, ɗanki na fama ne da wata cuta mai hana yaro girma, kuma da ke shafan ƙwaƙwalwar yara. Ita wannan cutar tana kama yara ne a cikin shekarunsu uku na farko, sannan tana shafan yadda ƙwaƙwalwar yara ya kamata ta riƙa yin aiki, da kuma yadda zai riƙa koyon magana. Sannan kuma wani yanayi ne mai wahala da a yanzu haka yake shafan ƙwaƙwalwar yara a nahiyar Afirka, inda har yanzu mutane ba su gane yadda abin yake ba.

**Duduwa:** To Likita, ana iya warkar da wannan cutar?

**Likita:** Idan aka samu maganin da ya dace, ana iya inganta rayuwar waɗanda suka kamu, amma dai cutar ba ta warkewa kwata-kwata har ƙarshen rayuwar mutum. Yawancin waɗanda cutar ta kama su na iya zama cikin 'yan'uwansu ko kuma a ungwanninsu.

**Duduwa:** To yanzu kana nufin cewa haka Musa zai ta zama har ƙarshen rayuwarsa?

**Likita:** Kamar yadda na faɗa miki ne, idan aka samu maganin da ya dace za a iya inganta rayuwarshi, amma dai babu tabbas cewa zai warke kwata-kwata. Sai na gwada shi sosai tukuna, sannan in gane cewa ko cutar ce ta kama shi. A yanzu haka ana ta gudanar da bincike a kan wannan cutar. Kuma abin da nake so ki sani shi ne cewa, ba Musa ba ne kawai ke da irin wannan matsalar. Akwai dubban yara da yawa da irin wannan cutar take damunsu. Cutar kuma ta fi kama yara maza fiye da mata. Sannan kuma duk da cewa babu wani taƙamaimen yawan mutanen da wannan cuta ta kama su a duniya, ƙiyasi ya nuna cewa mutane ɗaya zuwa biyu a cikin mutane dubu na da cutar. Kuma yawan mutanen da ke da cutar na ƙaruwa sosai a 'yan kwanakin nan.

**Duduwa:** Hmm... To me yake jawo ta? Ko dai maita ce kamar yadda maƙwabtana suke tunani? Ko kuma aljanu ne kamar yadda ni nake tunani? Me ya sa haka yake faruwa?

**Likita:** Har yanzu ba wata wata taƙamaimiyar amsa a kan abin da yake jawo ta. An kawo dalilai da yawa, amma ƙwararru ba su yarda da su ba. Wasu suna ganin cewa haihuwar yara ne bayan an tsufa. Amma wasu kuma suna ganin cewa ana gadon cutar ce daga kakannin-kakanni da kuma irin

yanayin da mutane ke zama a ciki. Amma dole in ƙara da cewa, har yanzu ba a gane taƙamaimen abin da yake kawo cutar ba.

**Duduwa:** Wato dai wannan wani bala'i ne kawai. Wani daga cikin zuri'ata ya aikata wani mummunan abin, yanzu kuma ɗana ne yake shan wahalar abin da aka aikata.

**Likita:** Malama, ni ba ina faɗa miki abin da za ki yarda da shi ba ne. Ni masani ne kawai a kan hallayar ɗan Adam kuma aikina shi ne in yi miki bayanin halin da ɗanki yake ciki. Iyakar abin da zan iya faɗa miki ke nan. Kina iya kawo min shi gobe don in ƙara gwada shi sosai. Kuma da zaran na gane halin da yake ciki, sai mu fara ba shi magani. Amma tun da har ya kai shekaru goma sha shida, yana yiwuwa maganin ya yi aiki ko kuma ya ƙi yi.

**Duduwa:** Na gode Likita. Amma ka yi haƙuri na ɓata maka lokaci da yawa, kuma akwai layi mai tsawon gaske a waje.

**Likita:** Kar ki damu. Shi kuma layin kullum ƙaruwa yake yi, a yayin da kuma kullum kayan aiki raguwa suke yi. Na gode, sai an jima.

**Mai ba da labari:**

An gudanar da ɗan bincike a kan yadda wannan ciwo da yake shafar ƙwaƙwalwar yara ya yaɗu a nahiyar Afirka. Amma dai abu ɗaya ya tabbata: wannan matsala ta ƙwaƙwalwa na ƙara kama mutane sosai. Barinsu ofishin likitan ke da wuya, sai aka fara ruwa. Har ila yau dai duk a cikin wannan gari, Amina na tsaye a ƙofar ɗakin ƙawarta Dije. Ruwa ya yi mata duka, kuma tana ta rawar ɗari.

**Fitowa ta 2: A makaranta**

**Amina:** Dije! Dije, buɗe ƙofar!

**Dije:** Wane ne? Gari bai gama wayewa ba. Ga ni nan zuwa.

**Amina:** Na dawo miki da rigarki, Dije.

**Dije:** Amina! Ikon Allah, na ji daɗin ganinki. Kin ba ni tsoro jiyan nan da na gan ki a kan titi. Sai kuma kika gudu. Ban san cewa kin iya gudu haka ba. Amma ki shigo mana! Shigo ciki. Ya kamata ki sa kaya a jikinki.

**Amina:** Ni zan wuce ne. Ba zan daɗe ba.

**Dije:** Amina, ba wani abu ai. Bai kamata kina jin tsoro ba. Babu abin da zai same ki tun da kina tare da ni, ina tabbatar miki da haka.

**Amina:** Ba wanda yake da kariya a nan. Babu. Sanyi na damuna. Na gaji, tsoro na kama ni.

**Dije:** Ai saboda kin daɗe jiya kina yawo a kan titi ne, ga shi kuma ana ruwa, sannan kuma duk kin jiƙe, Amina. Waye kuma ya ba ki wannan guntun burodin? Me zai hana ki yi wanka, kafin nan kin ga sai in haɗa miki abin da za ki ci. Yaya kika gani?

**Amina:** Hakan ya yi.

**Dije:** Yauwa! To ki shiga ki je ki yi wanka, ni kuma bari in fara haɗa miki *breakfast*, sannan in ɗauko miki kayan da za ki sa. Allah ya sa dai su yi miki daidai. Kin rame sosai! Yauwa Amina, bayan nan ina so in kin gama mu je mu ziyarci wani abokina. Kun taɓa haɗuwa. Amma dai bari mu gama wannan tukuna.

**Amina:** Shi ke nan. Na gode. Na gode ƙwarai da gaske.

**Mai ba da labari:**
A yayin da Dije take haɗa wa Amina abin da za ta ci kuma abin mamaki, Aminan na ta amincewa da duk abin da ta faɗa mata, shi kuma likita na can na ganin wani marasa lafiyan, wani matashi ne ɗan shekara ashirin da wani abu. Ku ci gaba da sauraro.

**Fitowa ta 3: A asibiti**

**Likita:** Mara lafiya na gaba! … Yauwa! Abokina, yaya sunanka kuma me ya kawo ka?

**John:** Sunana John. Na kawo kaina ne saboda saura kaɗan na kashe kaina.

**Likita:** To John, ɗan kulle ƙofar nan. Bai kamata a ce ana jin maganarmu ba. … Yauwa! To ina jinka, ka ce saura kaɗan ka kashe kanka? Ko za ka iya faɗa min me ya sa?

**John:** Labarin ya fara ne lokacin da na rasa aikina na kashiya. Ogana ne ya zarge ni da satan kudi, bayan ba ni ba ne. Na yi ƙoƙarin in yi mai bayanin cewa ni ban san da maganar ba amma ya ƙi saurarona.

**Likita:** Tun yaushe haka ne ya faru?

**John:** Kusan wata biyu ke nan. A lokacin matata tana da cikinta na farko. Ta haifi 'ya mace kwanan nan.

**Likita:** Ashe abu ya yi kyau ke nan. To ina taya ka murna! Yanzu ashe ka zama baba ke nan.

**John:** Haka, amma kuma baban da bai da amfani ba. Ban ga amfanin rayuwa ba. Ban taɓa samun kaina a cikin wannan halin ba. Kamar rayuwar ba ta da wani amfani a gare ni.

**Likita:** Na'am, to John me ka fi sha'awa a lokacin da ba ka komai?

**John:** Nakan je coci da matata don mu yi waƙa. Ina sha'awar yin haka sosai, amma ban da yanzu. Ba inda nake zuwa tun lokacin da na rasa aikina, sai sau biyu kawai da na fita, lokacin da matata za ta haihu da kuma lokacin da fastonmu ya ba ni shawarar in zo in gan ka, lokacin da ya ja ni muka fita.

**Likita:** To lallai John, na ji daɗi da ka yarda ka zo. Ba wani abu ba ne yake damunka illa takaici, sannan ya yi kyau da ba ka kashe kanka ba. Ana iya warkar da ciwon takaici, kuma za ka iya ci gaba da jin daɗin rayuwarka kamar yadda ka saba. Amma dole sai ka mai da hankali wajen kulawa da za mu riƙa ba ka kowane lokaci, sannan kar ka karaya idan ka ga kamar ba ka samun canjin nan take.

**John:** Gaskiya ne. To maganar aiki fa? Zan ƙara samun wani aikin?

**Likita:** Ɓan ga abin da zai hana ba.

**Mai gabatarwa:**

Da haka kuma muka kawo ƙarshen wannan shiri na yau. Sai kuma mun sadu da ku a shiri na gaba domin jin irin abubuwan da za su biyo baya. Kafin nan ana iya kasancewa da mut a adireshinmu na yanar gizo a dw.de/lbe domin sauraron wannan shirin. Kazalika kuna iya mahawara a shafinmu na Facebook. Sai mun sadu a shiri na gaba. Ku huta lafiya.